**KOMAI NISAN JIFA …**

**EPISODE 16**

**<u>Characters</u>**

*Alh. Bature*

*Husseini*

*Eze*

*Safiya*

*Jummai*

*Hassan*

**<u>Scene I</u>**

**NORTHERN KADUNA, ALH. BATURE'S SHOP**

1. **MUSIC:** **<u>THEME MUSIC</u>**
2. **SFX:** **<u>SOUND OF PEOPLE TALKING OFF MIC IN THE BACKGROUND.</u>**
3. **HUSSEINI**: **(OFF MIC)** Assalamu Alaikum! Assalamu Alaikum!
4. **ALH. BATURE:** **(ON MIC)** Wa'alaikumus Salam… Husseini ashe kaine.
5. **HUSSEINI**: **(RESPECTFULLY)** E yallabai neni, yaya gida ya iyali?
6. **ALH. BATURE**: Alhadilla muna lafiya. **(IMPATIENTLY)** Toh, Mallam Husseini, me ke tafi da kai, ko ka zo ka duba ni yau?
7. **HUSSEINI**: **(LAUGHS NERVOUSLY)** Erm, erm, na kawo kudin kayakin da na ansa kwanakin baya ne.
8. **ALH. BATURE**: Da kyau kwarai, husseini.
9. **HUSSEINI**: **(HESITATINGLY)** er.. Alhaji, zan so ka kara bani wasu kayan a bashi kuma .

10. **ALH. BATURE:** **(CONFIDENTLY)** Toh ai ba matsala ai… amma….Husseini, ko danuwanka Hassan ya janye takarar sa ne?

11. **HUSSEINI**: **(NERVOUSLY)** Em…..em….em wallahi Alhaji tauren kai yake yi. Ya ki janye takarar kememe, amma ba matsala zan saki masa magana
.

12. **ALH. BATURE**: **(UNHAPPILY)** gwada kam ka yi masa Magana…wai shin me yasa ya tsani ne haka bayan duk taimaka maka da nake yi, amadadin ya kyautata min?

13. **HUSSEINI**: **(QUICKLY)** Haba Alhaji Bature, na san Hassan ba tsananka yake yi, don Allah ka daina fadar haka.

14. **ALH. BATURE:** **(QUICKLY)** Husseini ka tabbata? Saboda ba hakan yake nuna waba fa .

15. **HUSSEINI**: Don Allah Alhaji ka manta da wannan, bara ma in sake tabbatar maka cewa dukan yanuwa na da iyali na suna jin dadin taimakon da kake yi min.

16. **ALH. BATURE**: **(NONCHALANTLY)** Toh ina fatan abin da kake fada hakan ne. saboda duk tallafin da nake maka da zuciya daya ne, kuma nasan zaka bukaci hakan ta ci gaba

17. **HUSSEINI**: **(CONFUSED)** ah! Alhaji me kake nufi da hakan? Don Allah kada ka fadi haka, ai bazai ma kai hakan ba.

18. **ALH. BATURE**: Eh toh… Husseini ko kai ai ya kamata kasan, ba daidai bane in cigaba da taimaka ma wani yanuwan abukan hammaiya, ai sai ayi shakar aminci na

19. **HUSSEINI**: Haba Alhaji, ba wanda zai yi tunanin hakan, yallabai..

20. **ALH. BATURE**: **(BRISKLY INTERRUPTS)** Kai Husseini, me ka maida ne, kada ka raina min wayo mana, jama'a su soma zuwa suna tambaya na

21. **HUSSEINI**: **(PLEADINGLY)** bah aka bani yallabai, don Allah ka gani mana…. …

22. **ALH. BATURE**: (**IMPATIENT**) Husssini bari in gaya maka, bani da lokacin wasa, yanzu mastayi na a gare ka da sauran yanuwan ka shi ciniki na akawo min kudi a dauka, na janye dukan taimakon da nake yi maka idan har danuwan ka bai janye daga takarar ba.

23. **HUSSEINI**: **(DISTRAUGHTLY)** Haba Alhaji, kada kayi haka mana yallabai!

**24. MUSIC:** **<u>BRIDGE MUSIC</u>**

<u>**Scene 2**</u>

**NORTHERN KADUNA: HAJIYA INNA'S COMPOUND EVENING**

**25. SFX:** **<u>SOUNDS OF CLINKING PLATES AND SPOONS.</u>**

26. **HASSAN**: **(ON MIC)** Jummai nita, wai da menene kika girka wanan abincin, yayi dandano kwarai.

**27. JUMMAI**: **(DOWN)** Hmm Hassan, *mai gida,* nayi murna kana jin dadin abincin **(SIGHS HEAVILY)**

28. **HASSAN**: Jummai, wai menene ke damun ki, fuskan ki ba fara ko kadan tun dazu

29. **JUMMAI**: **(SIGHS)** Ba wane abu bane fa, makarantar yaran nan ne suka kara kudin makaratar har ma kamar an ninka, abin dake damuna kenan

.

30. **HASSAN:** Kai, yayi yawa kam, basu san samun kudin da wuya bane yanzu?

31. **JUMMAI:** Sun ce wai suna son su gyara makarartar. Amma basu tunanin ina zamu same kudin

32. **HASSAN**: Kada ki damu kanki, duk da cewan su ninka kudin makarartar nafi son yaran su cigaba da karatu a makarartar, saboda suna bada ingantancin ilimi

33. **JUMMAI:** **(SOUNDING WORRIED)** Hakika gaskiyar ka, makarartar na daya daga cikin makarartun daga ake yabawa a duk garin nan, suna koyar da tarbiya suna kuma bada ingantancin ilimi .

34. **HASSAN:** Mhn… kin gani kenen masoyiyata

35. **JUMMAI:** **(SOUNDING WORRIED)** Amma Hassan mun sanye kudadin mu gaba daya cikin hidimar zaben da ke gabatowa, ina zamu same kudin biyan kudin makarartar?

36. **HASSAN:** Haba masoyita, ai muna iya amfani da ajiyar mu don biyan kudin makarartar yaran ai, bayan haka ma na sami kwangilar dinka wa wata maaikata ulifam, na sam zamu same wasu dan kudi

37. **JUMMAI:** (**SOUNDING RELIVED)** Na ji dadin kwarai tunda kana iya yin dan ajiya, ai sai godiya ma hanyan tazarar haihuwa da ta bamu damar shiri ma gaba .

38. **HASSAN:** E mana, ai saiya sa ma na ce muyi hakan

39. **JUMMAI:** **(HAPPILY)** Ai sai yasa na ke sonka, kullun kana nazari da shiri akan abubuwan da suka shafe iyalin mu

40. **HASSAN**: Kada ki zole ne mana,Jummai kinsa haka na faruwa ne saboda kina tare da ne

41. **JUMMAI:** **(HAPPILY)** Dama masu iya magana sunce, kamilum mace ai sai da mata.

42. **HASSAN:** Ah Jummai, kin goya min baya a dukan abinda nay i niyan yi, Allah saka miki, nagode

43. **JUMMAI:** *mai gida Nagode nima* **(SERIOUS)** Amma Hassan, menene kake ganin ya dace muyi game da matsallar dake tsakanin Husseini da Alhaji Bature?

44. **HASSAN:** **(INDIFFERENTLY)** Ah Jummai, menene za mu iya yi? Ai bai dace ace Alhaji Bature ya takura Husseini haka har takai ga kafa masa takunkumi ba.

45. **JUMMAI:** Mai gida na sani, nima nay i Magana ne saboda jama'a sun soma yadda jitajita a cikin gari, kuma hakan ba kya….

46. **HASSAN:** Jummai abar kaunata, bari in fada miki abu guda da yakamata kisani, mutane sai sun yada jitajita, ai damukradiya muke, ina laifin inyi takara da dan takarar da Alhaji Bature ke goya ma baya, idan ya kada ni ai shike nan, ai kujeran bana gadon gidan kowa bane

47. **JUMMAI:** *Toh* maigida, idan kana ganin hakan yafi shikenan…

48. **HASSAN:** **(CONFIDENTLY)** Jummai bari in fada miki dama duk saurar jama'a, ni bazan janye takara ta ba, duk da cewa Husseini na ta rook na in janye. Bana son makirci da kin gaskiya .

49. **JUMMAI:** **(PLEADINGLY)** toh, maigidana, kadai yi nazari sosai kafin ka dau kowace mataki, ba dace ku same sabani da danuwan kaba

.

50. **HASSAN**: **(NON-COMMITALLY)** Mhn naji

51. **HASSAN:** Jummai, bayan duk lokaci da kudaden da na saka a wannan takarar, menene keki son in yi? Ai wasu ma su aminci da ni.

**52. MUSIC:** **<u>BRIDGE MUSIC</u>**

**<u>Scene 3</u>**

**NORTHERN KADUNA, HUSSEINI MAI SHAYI SPOT NEAR THE MOTOR PARK**

**53. SFX:** **<u>BUSY TRAFFIC, CAR HORNS BLARING AND MUSIC PLAYING</u>.**

54. **EZE:** **(OFF MIC)** Kai yaya kake abokina?

55. **HUSSEINI**: **(ON MIC)** Eze, ina lafiya. Don Allah zauna ka sha shayi.

56. **EZE**: **(COMING ON MIC)** Abokina nagode, ai abinda nake bukata kenan kafin inyi maka albishir.

57. **HUSSEINI:** Mhhn… haka ne? Toh don Allah Eze ka fada min albishir din dake saka fara'a haka

58. **EZE:** **(SIPPING HIS TEA)** Abokina, ina cikin nishadi kwarai yanzu sakamakon zaman da muka yi da kungiyar ta lafiya ta al'uma. Kai na ji dadin zaman, za su sake tura ne Habuja akan nazarin koyan hanyoyin tazarar haihuwa
.

**59. HUSSEINI:** **(HAPPILY)** Kai! Eze, nay i maka murna kwarai.

60. **EZE:** Ai baka kai ne farin ciki ba, gaskiya naji dadin yadda kai da mai Unguwa kuka dage har na yarda na shiga kungiyar duk da magangannun na karya da naji game da Laraba.

61. **HUSSEINI:** Abokina ina jin dadi tunda kana fahimtar faidar kungiyan

62. **EZE:** Husseini,wannan Laraban da wuya a same mace kamar ita, dukan abinda Tanko ya fada mana game da it aba haka bane.

63. **HUSSEINI:** **(AMUSED)** Eze, ka tabbata? ba kaine kadage cewa muguwar mayya ce?

64. **EZE:** **(LAUGHS)** Husseini mance da wance, ko ka san cewa ita nars Laraba ce ta soma nuna cewa ni na dace a tura Habuja in hallarci taron nan na

65. **HUSSEINI:** Kai!, nayi maka murna kwarai abokina.

66. **EZE**: Don Allah abokina k aka yi mana yindomi da kwai mu yi murnan abinnan kwarai.

67. **HUSSEINI**: Ayah! Kaya na duk sun kare, ba yindomi ba kwai anan. Saidai kaji katin Alhaji ka sayo sai in yi mana

68. **EZE:** **(SHOCKED)** Me kake nufi da ba kwai ba yindomi? Haka ake kasuwan ce ne? ai idan kayan ka sun kare, kamata yayi ka je ka sake sayo wa, ko ba haka bane?

69. **HUSSEINI**: Aboki na da hakorana zan sayo ne? sun kare ne saboda ban da ishashen kudin sayan dukan abinda nake bukata anan kuma in biya kudin wurin nan ba tare da an bini bashi ba?.

70. **EZE:** **(BEWILDERED)** Amma me yasa hakan ke faruwa? Ina Alhaji? Ina ce yana taimaka maka?.

71. **HUSSEINI:** Alhaji ya daina bani kaya da bashi, yanzu kawai sai dai in saya da kudi

72. **EZE:** **(SURPRISED)** Amma me ya faru har Alhaji ya shanja ra'ayin sa? Ai alhaji na kyauta maka da. Menene ya faru?

73. **HUSSEINI**: Hmm Eze, lallai mun dade bamu gamu ba. Kasan Alhaji ya fada min inyi kokari Hassan ya janye takarrar sa, tunda ban samu Hassan ya janye takarrar tasa bay a daina taimaka min.

74. **EZE**: **(SHOCKED)** Ah amma bai kyauta ba. Bai dace a ce yayi haka ba Husseini.

75. **HUSSEINI:** toh, Alhaji yayi min kokari kwarai, kuma na gane dalilin sa na rashin tausaya ma abokin hamanyan dauwan sa.

76. **EZE**: Husseini, me yasa kake tausaya ma Alhaji haka, bayan yada yayi maka?

77. **HUSSEINI**: (**RESIGNEDLY**) Toh Eze, menene zai iya yi?

78. **EZE**: Babu kam Abokina, na tausaya maka, amma kada ka gaji da kokarin Magana da Hassan ko za a ci nasara.

79. **HUSSEINI**: Eze nay i dukan kokari na amma yaki ya saurare ni

80. **EZE**: Ina ganin ka sake yi masa Magana kilar zai sake shawara

81. **HUSSEINI**: Gaskiya, ban yadda na shigo wannan tsaka mai wuya ba, Eze

82. **MUSIC**: **<u>BRIDGE MUSIC</u>**

**<u>Scene 4</u>**

**NORTHERN KADUNA: ALHAJI BATURE HOUSE NIGHT TIME.**

**83. SFX:** **<u>DOOR OPENS AND CLOSES</u>**

84. **ALH. BATURE:** **(OFF MIC)** Assalamu alaikum

85. **SAFIYA:** **(ON MIC)** Wa'alaikumus Salam, barka da dawowa Alhaji Bature.

86. **ALH. BATURE:** Mhn… Safiya, nag ode, yaya kike?

87. **SAFIYA:** Lafiya lau, don allah ga sobo kafin in kawo maka abinci ka, ko?

88. **SFX:** **(<u>SOUND OF JUICE BEING POURED IN A CUP</u>)**

89. **ALH. BATURE:** Madallah, kin san ina son sobo kwarai, gashi wannan yayi dadin kwarai.

90. **SAFIYA**: Na san kana son sobon ne yasa nayi wannan musamman saboda kai.

91. **ALH. BATURE:** **(LOWERING HIS VOICE)** Matata, kyale abincin nan yanzu. Kizo ki zauna anan, kin san bana jin yinwar abinci yanzu….

92. **SAFIYA**: Er, Alhaji, kasan ba lokacin da ya dace mu sadu bane wannan

93. **ALH. BATURE:** **(SHOCKED)** Me kike nufi, Safiya?

94. **SAFIYA**: Alhaji, kasan abin da nake nufi, yakamata mu sake jinkirtawa dan kadan

95. **ALH. BATURE:** **(UPSET)** Amma Safiya, ina ce tunda asibitin sun ce baki da matsala ya dace ace kina dauke da juna biyu yanzu.

96. **SAFIYA**: **(GENTLY)** Alhaji, sai ka sake hakuri fa, kilar yakamata mu je asibitin mu tattauna da su, suyi mana bayani ko su bincika mu idan ta kama

97. **ALH. BATURE:** **(RISING HIS VOICE IN AN UPSET MANNER)** Kina son in je gwaji? Baki da hankali. Wata kilar ma ki sa sun yi karya a sakamakon gwajin ki ne ma

98. **SAFIYA:** **(ANGRILY)** Alhaji bai dace ace ranka n abaci game da zance nan ba. Na fada maka mu je tare amma ka ki kyimeme. Kodai kasan abida ke damun kane?

99. **ALH. BATURE:** **(UPSET)** Toh me kike nufi da hakan, Safiya?

**100. MUSIC:** **<u>THEME MUSIC</u>**